Ya Abu Zarr idan zaka dafa romo to ka yawaita ruwansa, ka bibiyi maƙotanka da shi

Daga Abu Zarr - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ya Abu Zarr idan zaka dafa romo to ka yawaita ruwansa, ka bibiyi maƙotanka da shi".

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kwaɗaitarwa Abu Zarr al-Gifari - Allah Ya yarda da shi - cewa idan zai dafa romo to ya yawaita ruwansa, ya bibiyi maƙotansa da shi.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5336